*KASHI NA DAYA KWANAKIN YESU NA KARSHE*

Darasi na1

# YESU, MAFIFICIN DUTSE NA ALLAH

Luka 2:1-7, 41-52; Yahaya 20:31

**Bulok na Ginin Allah:**
**Yesu shi ne mafifificin Dutse na Allah.**



**ME MUKE SO YARA SU KOYA A WANNAN DARASI?**

Za su:

* danganta ra'ayin gina gida da shirin ginin Allah domin cetonmu da Ikilisiyarsa.
* gane cewa zuwan Yesu da mutuwarsa su ne mafificin dutse domin shirin Allah ya kawo ceto ga duniya.

**HADDACEWA**

"Ga shi, na sa mafificin dutsen gini a Sihiyona, zababbe, daukakakke. Duk mai gaskatawa da shi kuwa, ba zai kunyata ba."

1 Bitrus 2:6

## SHIRIN MALAMI



### *NAZARIN LITTAFI MAI TSARKI*

Tuna fa, darasan wannan shekara sun karfafa zancen **gini** ne. Da fari za mu dubi karshen rayuwar Yesu a duniya, da mutuwarsa da tashinsa, da komowarsa sama. Za mu ga cewa shirin Uban ne ya yi amfani da zuwan Yesu don ya kawo ceto ga dukan mutane. Za mu ga cewa Yesu shi ne Dutse Mafifici na shirin Allah domin kawo ceto ga dukan mutane. Labaru na Ayyukan Manzanni sun nuna yadda Allah ya fara gina Ikilisiyarsa.

Darasi na 1 ya gabatar da kan magana "gini" na darasan wannan shekara. Idan an taimake su yin tunani a kan yadda ake gina gida, zai shiryad da su su fahimci abubuwan da ke darasai na wannan shekara.



### *ME AKE BUKATA DOMIN DARASIN NAN?*

1. Hoto na 1, 'Yesu ya aikata mu'ujizai' domin Labari Daga Littafi Mai Tsarki Kashi na 3.
2. Domin GABATARWA, kayan aikin gini. Wanda ya san wani abu a kan gini ya fada wa yara wani abu a kan gini. A kai su inda za su ga ana gini.
3. Domin Labari Daga Littafi Mai Tsarki Kashi na 3, kawo littafi na 2 ko wasu hotuna na ayyukan Yesu da mu'ujizansa.
4. Domin KARSHEN DARASI, igiya ko zaren da ya kai kafa 6; felen takardar A-4, 2. Nade kowannensu biyu. Rubuta 'Haihuwar Yesu' a kan dayansu. A kan dayan rubuta, "Yesu ya koma sama." (Dubi shafi na 5.)



## LOKACIN DARASI

**A FARA DA ADDU'A**

**Gabatarwa**

- NUNA kayan gini da ka kawo. Yayin da kana nunawa, yara su fadi sunayensu da aikinsa. FADI yadda ake gina gida ko wasu abubuwa. Yi tambayoyi a kan gini, kamar— *Wanene ya taba gani ana gina gida? Ina yawan lokacin da za a dauka wajen gina babban gida mai karfi? Ban da kayan aikin da muna da su yanzu, wadanne abubuwa ake bukata don gina gida?*

- GABATAR da mutumin da ka kawo aji saboda ya yi magana a kan gini. Ya yi magana a kan gina gida. A lokacin da yana magana, sai ka rubuta matakan da za a dauka wajen gina gida. (Zana irin gida, tonon fandisha, sa duwatsu a kusurwa, gina sauran fandisha, sa katakan kofofi da sauransu. Ya karfafa batun mahimmanci dutsen kusurwa.) Idan zai yiwu, ka fitar da yara waje zuwa inda mutane ke yin gini.

- BAYYANA cewa a wannan shekara, labarunmu za su kasance ne a kan gine - gine iri-iri — Allah yana gina Ikilisiyarsa. Darasinmu na fari zai taimake mu yin tunani a kan yadda Allah ya kafa ginshikin gininsa. A darasin yau, za mu maimaita wasu abubuwan da kun rigaya kun sani game da zuwan Yesu da lokacin da yana girma.

## 1. A lokacin da Yesu ya zo (Luka 2:1-7)

- UMARCI yara su fadi wani abu a kan Kirisimati wanda ba da dadewa ba suka yi bukinsa. Yara su fadi wasu muhimman abubuwan da iyayensu suka yi a ranar Kirisimati. (Misali, cin abinci mai dadi tare, zuwa Coci a daren Kirisimati ko a rana Kirisimati, ba da kyautai da sauransu.)
- TUNA musu dalilin Kirisimati - domin tuna da zuwan Yesu duniya.
- RUBUTA bisa allo ayyuka da mutanen da sun shafi haihuwar Yesu. (Misali - Yusufu, da Maryamu suna zuwa Baitalami, makiyaya suna yi wa Yesu sujada, Hannatu da Saminu suna gai da Yesu a haikali, shehunan daga gabas za su yi wa Yesu sujada, gudu zuwa Masar, komowa Masar da zuwa Nazaret da sauransu.)

## 2. Yesu ya yi girma (Luka 2:41-52)

- TUNA masu abin da suka sani game da shekarun da Yesu yake girma:
  —Ya girma a birnin Nazaret, inda Yusufu babansa yake aikin kafinta. Ya taimaki babansa har shi ma ya iya aikin kafinta.
  —Iyalinsa talakawa ne, don haka mai yiwuwa ne suna da daki ciki daya tak.
  —Mai yiwuwa ya je makarantar 'yan maza wanda ke haikali inda malami ke koyar da su Dokar Tsohon Alkawari.
  —A gidansu, Yusufu yakan fada musu labarun mutanen Allah - Ibrahim, Yakubu, Musa da sauransu.
- Ba da labarin yadda Yesu da iyayensa suka ziyarci haikali (Luka 2:41-52).
- Tuna musu cewa Yesu yana nan kamar kowane yaro a Isra'ila a wancan lokaci. Amma kuma shi dabam yake ta wata muhimmiyar hanya - Bai taba yin zunubi ba! Karanta Luka 2:52.

## 3. Yesu ya fara aikinsa

- KARANTA Luka 3:23a.
- NUNA hotuna daga littafi na 2 na mu'ujizan Yesu. Yi tambayoyi a lokacin da kana nuna su don maimaita ayyukan da Yesu ya yi a lokacin da ya fara aikinsa a duniya.
- NUNA Hoto na 1.
- KARANTA Yahaya 20:31. BAYYANA cewa Yesu ya yi amfani da mu'ujizansa don ya nuna wa mutane Ubansa kuma ya kawo su su ba da gaskiya gare shi, hanya daya tak zuwa samun rai madawami. Rubuta a kan allo; "Yesu ya zo domin mu sami rai."

## 4. Yesu shi ne Mafificin Dutse (1 Bitrus 2:6-8)

- TUNA musu matakan gini kamar yadda muka ji a gabatarwa. Mataki na fari shi ne a zana irin abin da za a gina sai kuma kafa harsashin gini. Allah ya aiko Yesu duniya saboda ya biya zunuban dukan mutane ta wurin mutuwarsa.
- NUNA babban bulok ko dutse da ya zama "mafificin dutse." KARANTA 1 Bitrus 2:6. Bitrus ne ya rubuta wannan aya. Ya dauko daga Tsohon Alkawari. Bitrus yana nufin Yesu ne a lokacin da ya rubuta wadannan kalmomi.
- BAYYANA cewa a wasu darasai a nan gaba, za mu koyi wasu abubuwa a kan rayuwar Yesu na karshe kafin ya mutu. Za mu ga cewa dukan abubuwan da suka faru da Yesu, sun faru ne a matsayin shirin Allah don kawo ceto.

## Karshen Darasi...

* Yara 2 su rike karshen zaren da ka kawo. Bayyana cewa za mu mori zaren don mu nuna rayuwar Yesu, kafin mutuwa da bayan ya mutu. Rataya takardun ayyukan nan 2 (**Haihuwar Yesu, komawar Yesu sama**) a bakin zare. Ayyukan nan da za mu koya sun faru ne bayan haihuwar Yesu kuma kafin ya koma sama.

► **Koyar da Haddacewa yanzu (1 Bitrus 2:6).**

**ADDU'A:** Karfafa yara kima su yi addu'ar godiya saboda zuwan Yesu a duniya da ayyukan al'ajabi da ya yi. Gode wa Yesu saboda ya zo duniya ya bamu rai da ceto.

**WAKA:** "Yesu dutsen cetona..." ♫

**Bulok na Ginin Allah:** ***Yesu shi ne Mafificin Dutse na Allah.***